# SŪRATUL MĀ‘ŪN سُورَةُ المَاعُونِ

Tana bayãnin yadda zã a iya gãne munãfuki da halãyensa a tsakãnin Musulmi.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Shin, ka ga wanda ke ƙaryatãwa game da sakamako?

*2.* To, wannan shi ne ke tunkuɗe marãya (daga haƙƙinsa).

*3.* Kuma bã ya kwaɗaitarwa bisa bayar da abinci ga matalauci.

*4.* To, bone yã tabbata ga masallata,

*5.* Waɗanda suke masu shagala daga sallarsu,

*6.* Waɗanda suke yin riya (ga ayyukansu)

*7.* Kuma suna hana taimako.

أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ ١

فَذَٰلِكَ ٱلَّذِى يَدُعُّ ٱلْيَتِيمَ ٢

وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلْمِسْكِينِ ٣

فَوَيْلٌ لِّلْمُصَلِّينَ ٤

ٱلَّذِينَ هُمْ عَن صَلَاتِهِمْ سَاهُونَ ٥

ٱلَّذِينَ هُمْ يُرَآءُونَ ٦

وَيَمْنَعُونَ ٱلْمَاعُونَ ٧